The Kumbotso Teacher Educator (KUTEJ): A Journal of Multidisciplinary Studies
Volume 5.1 January 2014 ISSN: 1597-8796

# SARAUTAR XANRIMI A MASARAUTAR KANO

***Garba Saleh***
Kwalejin Ilimi Ta Amana, Qunchi
(ACOE QUNCHI KANO)

## Tsakure

*Wannan takarda mai taken Sarautar Xanrimi a Masarautar Kano, an shirya ta ne da nufin bincikowa tare da bayyana asalin samuwar wannan sarauta mai matuqar muhimmanci a kan sha'anin Fada. Hanyoyin nema da kuma tattara bayanan binciken sun haxa da karance-karancen rubuce-rubucen da suke da nasaba da fada, musamman ta Kano, da tattaunawa da mutanen da suka san fada da kuma ziyartar fada domin lura da sha'anoninta musamman waxanda suka shafi sarautar Xanrimi. Sakamakon binciken ya zo da salsalar sarautar Xanrimi da waxanda suka riqe ko suke riqe da sarautar da ayyukan basaraken da makusantansa, kamar hakimai, da kuma matsayin sarautar a Masarautar Kano.*



## Gabatarwa:

Sarautar Xanrimi xaya ce daga cikin sarautun manyan bayi a masarautar Kano. Sarautun bayi sarautu ne masu matuqar muhimmanci da tasiri wajen tafiyar da sha'anin mulki.

Matsayin manyan bayi irin su Shamai da Xanrimi da Sallama da Sarkin Dogarai da sauransu a idanun jama'ar gari da ma iyayen gidansu muhimmi ne, wannan ce ma ta samar da sarautun bayi iri daban-daban, tun zamani mai tsawon gaske. Manya daga cikin sarautun bayi a masarautar Kano sun haxa da Shamaki da Xanrimi da Sarkin Dogarai da Sallama da Kilishi da Sarkin Hatsi. Da sauran su. Daga ciki wannan takarda ta keve sarautar Xanrimi domin yin tsokaci da nufin nusar da jama'a game da ita.

## Asalin Samuwar Sarautar Xanrimi A Masarautar Kano

Sarautar Xanrimi na xaya daga cikin sarautun bayi a fadar Kano. Ita ce ta biyu ta fuskar matsayi a jerin sarautun manyan bayi.

Sarautar Xanrimi daxaxxiyar sarauta ce a masarautar Kano. Bincike ya tabbatar da cewa tun kafin zuwan sarakunan Fulani akwai bayi a masarautar Kano, sai dai ba maganar muqami ake yi ba, maganar bautar kawai ake yi. Amma babu maganar muqami irin na Shamaki da Xanrimi da Sallama da Kilishi da Sarkin Dogarai da dai sauran su. (MDAM 08/06/2005)

An samu ra'ayoyi mabambanta dangane da asalin samuwar wannan sarauta ta Xanrimi. Wasu daga cikin ra'ayoyin sun

danganta samuwar ta da zamanin sarakunan Have. Akwai kuma ra'ayoyi masu cewa ta samo asali ne zamanin sarakunan Fulani. Daga cikin waxannan ra'ayoyi akwai:

Ahmad (2001: 129) ya bayyana cewa sarautar Xanrimi ta samo asali ne zamanin sarakunan Have a zamanin Sarkin Kano Abubakar (1565 – 1673). Ya bayyana cewa akwai wani yaro mai suna Isa xan wani bawan Sarki mai suna Ali Gadanga (Sarkin Tarko). A lokacin da Isa yake yaro, duk yayin da ya fito wasa ba shi da wurin wasa sai kan itaciyar rimi da take gidan Sarki. Wannan ta sa duk lokacin da mahaifiyarsa ta fito neman sa, takan ce masa "Kai dai ba ka da wurin wasa sai kan itaciyar rimi, ka dai zama xan rimi".

Kasancewar sa xanta na fari, wanda a al'adance ba a faxar sunansa, sai ta riqa kiransa da Xanrimi, har sunan ya bi shi. Bayan ya girma, sai Allah ya sa wa Sarkin Kano Abubakar son sa. Saboda haka, sai ya yi masa sarauta, sai aka riqa kiransa da Xanrimi.

Shi kuwa Sadauki (30/03/98) ya bayyana cewa an yi wani bawan Sarki mai suna Barka. Zamanin sarkin Kano Sulaiman (1807-1819). Wata rana sai ya ce wa Sarkin Kano Ibrahim Dabo (Kafin ya zama Sarki) "Na yi has ashen cewa nan gaba za ka shahara ka bunqasa, ka yi qarfi kamar bishiyar rimi". Nan take shi kuma, sai ya mayar masa da cewa: "In dai har na zama kamar bishiyar rimi, to ni kuma zan tafi da kai a matsayin Xanrimi".



Bayan Allah ya nufi Ibrahim Dabo da zama Sarkin Kano (1819-1846), sai ya cika alqawarinsa, in da ya naxa wa Ibrahim Barka Sarautar bayi, ya kuma kira sunan Sarautar Xanrimi.

Saboda haka, ta la'akari da waxannan ra'ayoyi da suka gabata, za a iya cewa Xanrimi na farko shi ne Xanrimi Isa zamanin Sarkin Kano Abubakar (Zamanin Sarakunan Have) ko kuma Xanrimi Barka zamanin Sarkin Kano Ibrahim Dabo.

Bincike ya tabbatar da cewa, wannan sarauta ta Xanrimi ta fara wanzuwa ne zamanin Sarkin Kano Ibrahim Dabo, kamar dai yadda ra'ayi na biyu ya bayyana, domin tun daga wannan zamani ne aka samu cigaba da wanzuwar wannan sarauta har ya zuwa yau (Anold 1999:133).

Xanrimin Kano na farko shi ne Ibrahim Barka, wanda aka naxa shi bayan jihadin Shehu Usman Xanfodiyo, zamanin Sarkin Kano Ibrahim Dabo (1819-1846), har zuwa a zamanin Sarkin Kano Usman I. Bayan ya tsufa ne, sai aka tuve shi, aka naxa xansa Malam Barka, zamanin Sarkin Kano Usman I. wanda shi ma aka tuve shi bayan shekara xaya tak, sakamakon savanin da ya samu tsakaninsa da Sarkin Kano Abdullahi Maje Karofi.

Daga nan ne sai aka naxa xan'uwansa Xankaka a matsayin sabon Xanrimi. Wanda shi ma aka tuve shi bayan ya yi shekara takwas a kan wannan muqamin, sakamakon savanin da ya riqa afkuwa tsakanin iyalan marigayi Xanrimi Barka da Sarkin Kano Abdullahi Maje Karofi (CSMM 07/06/96).

Bayan nan sai aka naxa wani bawa mai suna Salam (buzu daga Tunis) a shekarar 1867, wanda ba shi da wata alaqa da gidan Xanrimi Barka, kuma kafin naxin nasa yana riqe ne da sarautar Sarkin Littafi (AMK 09/03/98).

Bayan Xanrimi Salam, a qarshen zamanin Sarkin Kano Abdullahi Maje Karofi, sai aka naxa Hamza a matsayin sabon Xanrimi wanda shi ma xa ne ga Xanrimi Barka. Daga nan sai aka naxa Yahaya a zamanin Sarkin Kano Muhammadu Bello, wanda ya riqe har zuwa zamanin Sarkin Kano Muhammadu Tukur.

Amma bayan yaqin basasar Kano, sai aka tuve shi. Daga nan sai aka naxa Nuhu a matsayin sabon Xanrimi zamanin Sarkin kano Aliyu (1894-1903), wanda shi ma ya riqe muqamin har zuwa lokacin da Turawa suka zo a shekarar 1903.

Bayan Turawa sun naxa Abbas a matsayin sabon Sarkin Kano (1903-1919), shi kuma sai ya naxa Allah Bar Sarki a matsayin Sabon Xanrimi. Xanrimi Allah Bar Sarki ya shahara matuqa, wanda daga baya har sai da ya yi Wazirin Kano. Hakan kuwa ya faru ne bayan da Turawa suka tuve Wazirin Kano Abdullahi Bayero a shekarar 1908. Amma daga qarshe su da kansu (Turawan) suka tuve Xanrimi Allah Bar Sarki. Suka kuma tura shi gudun hijira (Sufi, 1993: 132).

Bayan wannan ne, sai aka naxa Sambo a shekarar 1910, zamanin Sarkin Kano Abbas, Xanrimi Sambo ya riqe wannan sarauta har zuwa zamanin Sarkin Kano Usman II. Bayan an tuve shi ne, sai



aka naxa Mamman a matsayin Sabon Xanrimi, wanda daga baya shi ma Turawa suka tuve shi, suka kuma tura shi gudun hijira.

Tun daga wannan lokaci, ba a sake naxa wannan sarauta ba, har sai zamanin Sarkin Kano Sir, Muhammadu Sunusi (1953 – 1963). Sai aka naxa Muhammadu a matsayin sabon Xanrimi, wanda ya riqe har zuwa zamanin Sarkin Kano Muhammadu Inuwa.

Daga Xanrimi Muhammadu, sai aka naxa Shehu a matsayin sabon Xanrimi, zamanin Sarkin Kano Alhaji (Dr.) Ado Bayero. Bayan rasuwarsa, sai aka naxa Abdulqadir, wanda Allah ya yi wa rasuwa a shekarar 2004. Bayan rasuwarsa ne aka naxa Wada Najolo a matsayin sabon Xanrimi. Yana kan wannan matsayi ne aka xaga likkafarsa zuwa matsayin Shamakin Kano har ya zuwa wannan lokaci.

Bayan an xaga likkafarsa zuwa matsayin Shamakin Kano, wanda ita ce sarauta mafi girma a sarautun bayi, sai aka naxa Xanrimi mai ci na yanzu, wato Xanrimi Sarki Waziri a shekarar 2013 (UK. 15/06/2014). Domin samun qarin haske dangane da bayanan da suka gabata a sama, sai a duba wannan jadawali.

Jerin Sunayen Waxanda Suka Riqe Sarutar Xanrimi da Sarakunan da Suka yi Zamani da su:

| S/N | XANRIMI | SARKI | SHEKARA |
|---|---|---|---|
| 1. | ……………… | Sulaiman | 1807 – 1819 |
| 2. | Ibrahim Barka | Ibrahim Dabo | 1819 – 1846 |
| 3. | Malam Barka | Usman I | 1846 – 1855 |
| 4. | Salam | Abdullahi | 1855 – 1883 |
| 5. | Hamza | Abdullahi | 1855 – 1883 |
| 6. | Yahaya | Abdullahi | 1855 – 1883 |
| 7. | Yahaya | Muhammad Bello | 1883 – 1892 |
| 8. | Nuhu | Muhammad Tukur | 1892 – 1894 |
| 9. | Allah Bar Sarki | Aliyu | 1908 – 1919 |
| 10. | Sambo | Abbas | 1903 – 1919 |
| 11. | Mamman | Abbas | 1903 – 1919 |
| | - | Usman II | 1919 – 1926 |
| | - | Abdullahi Bayero | 1926 -1957\3 |
| 12. | Muhammadu | Muhd.Sunusi | 1953 – 1963 |
| 13. | Shehu | Muhammad Inuwa | 1963 – 1963 |
| 14. | Abdulkadir | Ado Bayero | 1963 – 2014 |
| 15. | Wada Wajalo | Ado Bayero | 2004 – 2014 |
| 16. | Sarki Waziri | Ado Bayero | 2014 – - |
| 17. | Sarki Waziri | Sunusi Lamido Sunusi II | 2014 - - |

(Anold, 1991: 133)

Idan aka yi la'akari da wannan jadawali za a fahimci cewa wannan sarauta ta Xanrimi ta samo asali ne zamanin sarkin Kano Ibrahim Dabo zuwa yanzu mutane goma sha biyar ne waxanda suka riqa wannan sarauta.

**Xanrimi Da Ayyukansa**

Xanrimi yana xaya gada cikin qasaitattun bayi a fadar Kano. Sarautar Xanrimi kamar yadda bayani ya gabata, ita ce ta biyu a



muhimmanci a sarautun bayi bayan sarautar Shamaki. Sarautar Xanrimi a iya kiranta da babban xan tsaya, wanda Hausawa kan yi wa kirari da cewa "idan babu shi, babu kaxi". Domin kuwa ma fi yawan ayyukan da ake gudanarwa a fada da hannunsa ciki (XKWN 06/06/2005).

Sarautar Xanrimi, kamar sauran manyan sarautun bayi, Sarki ne yake da ikon zabensa, yakan kuma zabi wanda yake ganin ya amince masa ta fuskar gaskiya da rikon amana, hakan ta yi matukar tasiri a sarautar Xanrimi kamar yadda aka gani a baya. Misali, da yawa daga cikin 'ya'yan Xanrimi Barka sun yi wannan sarauta. Amma daga baya saboda savanin da aka riqa samu tsakanin zuriyar Xanrimi Barka da sarakunan Kano ya sa aka daina naxa zuriyarsa aka riqa naxa waxanda ba su ma gada ba, kamar Xanrimi Salim da Nuhu da sauransu.

Bayan Sarki ya zavi wanda za a naxa a matsayin Xanrimi, yakan bayar da kayan naxi, waxanda suka haxa da babbar riga da rawani xan Kura da Fatuma (Hula havar kada mai adon ulu) da alkyabba. A ranar naxin dukkan manyan bayi da hakimansa da ma makaxa da mawaqan sarki (Masarta) za su taru a soron tambari, a inda Sallama yake naxa shi.

Da zarar an gama naxi, sai sauran bayi su zo su yi gaisuwa, tabbacin cewa sun yi mubaya'a. Daga nan kuma, sai a cigaba da kaxe-kaxe da bushe-bushe, har a raka shi gida.

A al'adance, Shamaki da Xanrimi ba sa zuwa zaman fadanci, duk lokacin da Sarki yake fada, su kuma suna nasu zaman

fadancin da hakimansu. Ciroman Shamaki da Makaman Xanrimi su ke zama a fada a madadinsu. Amma a yanzu su ne suke zama da kansu don gudanar da ayyukan da suka shafe su.

Saboda haka, dangane da Xanrimi dukkan wasu ayyuka da suka shafe shi, Makamansa shi ne yake aiwatar da su. Idan kuma aka bayar da wani umarni wanda ya shafi gidan Xanrimi, sai shi Makaman Xanrimi ya je ya shaida masa cewa an yi kaza, an yi kaza. Idan kuma wani abu ne da ake buqatar aiwatarwa, Xanrimi yakan umarci waxanda abin ya rataya a wuyansu su aiwatar (OKIWN 08/06/2005).

Bisa al'ada, duk wasu muhimman al'amura da suka shafi sha'anin mulki, Sarki yakan tattauna da manyan bayinsa irin su Shamaki da Xanrimi da Sallama da sauran su, don neman shawarwarinsu.

Sarautar Xanrimi muhimmiya ce a masarautar Kano. Yana kuma da ayyuka masu yawan gaske da suka rataya a wuyansa domin aiwatarwa. Wannan ce ma ta sa aka amince masa ya naxa hakiman da za su rinqa taimaka masa wajen gudanar da ayyukansa. Hakiman da suke qarqashinsa sun haxa da:

1. Makaman Xanrimi
2. Madakin Xanrimi
3. Galadiman Xanrimi
4. Ciroman Xanrimi
5. Sarkin Fadar Xanrimi
6. Barden Xanrimi



7. Garkuwan Xanrimi
8. Shamakin Xanrimi
9. Turakin Xanrimi. Da sauran su (MDAM 8/6/2015).

Kafin a ci gaba da bayani a kan sarautar Xanrimi, bari a kawo ayyukan masu riqe da waxannan sarautu a taqaice don samun qarin haske.

**Makaman Xanrimi:**

Wannan shi ne babban mataimakin Xanrimi, yana kuma da gurbi yayin zaman fadanci. Muhimman ayyukan sa sun haxa da:

1. Gabatar da maqaraya maza a gaban sarki, domin jin koke-kokensu. Kuma shi ne yake gabatar da takardun alqalai zuwa gaban sarki, ko kuma daga sarki zuwa ga alqalai.
2. Bayan wannan kuma lokacin zaman Fada, majalisa gaba xaya a hannunsa take, shi yake da alhakin nuna wa kowane hakimi wajen zamansa.
3. Har ila yau, kuma a lokacin hawa yana daf da likkafar Xanrimi. Duk lokacin da sarki ya waiwayi Xanrimi da wani umarni, shi kuma nan da nan sai ya umarci Makaman Xanrimi don aiwatarwa. Haka kuma alhakinsa ne ya tabbatar cewa kowane hakimi ya tsaya a gurbinsa yayin hawa.
4. Ana iya tura shi wakilci zuwa garin wani hakimi idan ya mutu ko an dakatar da shi, kafin a naxa wakilci ko kuma kafin a sulhunta. A wasu lokutan kuma akan iya tura shi

ya kai saqo zuwa garuruwan hakimai ko ma wasu masarautun (MDAM 08/08/2015).

**Madakin Xanrimi**

Madakin Xanrimi shi ne mai kula da duk wani saqo da ya fito daga hannun sarki zuwa ga qananan hukumomi ko zuwa ga hakimai ko ma zuwa ga wasu masarautun. A tsarin zaman fada ba shi da gurbi, amma yakan je ko da wani saqo zai fito daga hannun sarki, nan da nan sai a kira shi a ba shi. A lokutan hawa kuma yana cikin giwar sarki. Shi ma ana iya tura shi wakilci zuwa garin wani hakimi.

**Galadiman Xanrimi**

Galadiman Xanrimi ba shi da gurbi yayin zaman fada, sai dai yakan halarta saboda shirin ko-ta-kwana. Ma'ana ko da wani saqo zai fito daga hannun sarki. Madakin Xanrimi yana iya umartarsa ya kai saqon. A lokutan hawa shi ma yana cikin giwar sarki. Za kuma a iya tura shi wakilci zuwa garin wani hakimin. Bayan wannan kuma Xanrimi yana iya umartar sa da ya gudanar da wasu aikace- aikace da suka shafi fada ko kuma kulawa da aikin wani idan ba ya nan.

**Ciroman Xanrimi**

Muhimman ayyukansa sun haxa da kai saqonnin sarki zuwa garuruwan hakimai ko ma wasu masarautun. Ba shi da gurbi yayin zaman fada, a lokutan hawa yana cikin giwar sarki. Yana



kuma daga cikin masu bin sarki idan za shi wani muhimmin al'amari a cikin gida. Misali buxe makaranta ko kuma bikin saukar karatu. A matsayinsa kuma na wanda yake qarqashin Xanrimi, Xanrimi yana iya umartarsa don gudanar da wasu ayyuka. Haka kuma ana iya tura shi wakilci zuwa garin wani hakimi.

**Sarkin Fadar Xanrimi**

Shi ma kamar Ciroman Xanrimi, ana tura shi wakilci. Yana kuma daga cikin masu kai saqonnin sarki zuwa garuruwan hakimai da ma wasu masarautun. Yayin da duk sarki zai yi tafiya a cikin gari ko qananan hukumomi ko jihohi maqwabta, yana daga cikin masu rufa masa baya. A lokutan hawa kuma, shi ma yana cikin giwar sarki. Shi ma kamar sauran Xanrimi na iya ba shi umarnin aiwatar da wani abu da ya shafi sha'anin fada.

**Barden Xanrimi**

Barde ba shi da gurbi yayin zaman fadanci, amma yakan halarta ko da wani saqo zai fito daga sarki wanda za a iya umartar sa don aiwatarwa. Shi ma kamar sauran ana iya tura shi wakilci. Yana kuma daga cikin masu kai saqonnin sarki zuwa garuruwan hakimai ko ma wasu masarautun.

**Garkuwan Xanrimi**

Daga cikin ayyukansa akwai kai saqonni zuwa garuruwan hakimai. Kuma a matsayinsa na yaron sarki za a iya tura shi

wakilci. Har ila yau, yana daga cikin masu rufa wa sarki baya yayin da zai yi tafiya. Yana kuma cikin giwar sarki a lokutan hawa, bayan wannan kuma Xanrimi yana iya umartar sa da ya gudanar da wasu ayyukan. Misali kula da aikin wani idan ba ya nan.

**Shamakin Xanrimi**

A matsayinsa na yaron sarki za a iya tura shi wakilci, sannan kuma yana daga cikin masu kai saqonnin sarki zuwa duk inda aka buqata. Bayan haka kuma yana daga cikin masu bin sarki yayin da zai halarci wani muhimmin al'amari. Bisa al'ada shi ne tsani tsakanin Xanrimi da duk mai son ganinsa a matsayinsa na Shamakinsa. Ma'ana babu wanda zai gana da Xanrimi sai ta hannunsa.

**Turakin Xanrimi**

Babban aikinsa shi ne kulawa da gine-ginen gidan sarki, duk abin da ya shafi aikin gini ko rufi ko wutar lantarki a hannunsa suke. Bayan haka kuma shi ne sarkin baqi. Duk baqon da aka yi yana qarqashin kulawarsa. Misali abin da ya shafi makwanci da abinci da ma duk wani abu da zai buqata.

A matsayinsa na yaron sarki, shi ma ana iya tura shi wakilci zuwa garin wani hakimi. A lokutan hawa yana cikin giwar sarki. Sannan kuma shi ma kamar sauran Xanrimi na iya umartar sa don ya gudanar da wasu ayyukan (DKWN 08/08/2015).



Kowane xaya daga cikin waxannan hakimai na Xanrimi, akwai yaran sarki marasa muqami a qarqashin su, kuma su ne tsani tsakanin su da Xanrimi. Duk wani abu da ya shafe su, ko wani umarni da za a ba su, dole ne ya biyo ta hannun iyayen gidansu. Haka abin yake idan wani abu suke nema a hannun Xanrimi, nan ma sai sun bi ta kan iyayen gidansu.

Wannan shi ne tsari tabbatacce, kowane daga cikinsu yana qoqarin kulawa da ayyukansa kamar yadda ya kamata. Babu mai ikon gudanar da aiki wani ko da kuwa ba ya nan, sai bisa umarnin Xanrimi ko Makaman Xanrimi.

A lokacin fadanci, ko kuma yayin da Sarki yake tafe a doki ko a qasa, Xanrimi yana vangaren hagunsa. Wannan ne ma ya sa ake yi masa kirari da:

**“Bahago Tausa Dama” (Saleh 2006)**.

Kamar yadda aka ambata, vangaren hagu nan ne bangaren Xanrimi. Xanrimi shi ne daf da likkafar Sarki, daga shi sai Makaman Xanrimi sai Madakin Kano sai Xanmaje sai Xankadai sai Falaki sai Xanmadami da sauransu. A wasu lokutan hakimai sukan ware ko su koma cikin yaransu a bar bayin kawai (MKASSY, 11/06/2005).

**Matsayin Sarautar Xanrimi Wajen Tafiyar Da Harkokin Mulki A Kano**

Ta la'akari da matsayin sarautar Xanrimi wajen tafiyar da harkokin mulki, za a ga cewa ayyukansa suna da yawan gaske, saboda duk wani muhimmin al'amari da za a gudanar da sa hannunsa. Wasu daga cikin muhimman ayyukansa sun haxa da:

Xanrimi yana daga cikin manyan bayin da suke fara tarar Sarki yayin da zai fito zaman fadanci. Shi ne babban mataimaki ga Shamaki. A duk lokacin da Shamaki ba ya nan, Xanrimi ne yake da alhakin gudanar da ayyukansa.

A zamanin Turawan mulkin mallaka shi ne jakada tsakanin Sarki da Razdan. Duk wani saqo daga Sarki zuwa Razdan ko kuma daga Razdan zuwa Sarki, dole sai ya biyo ta kan Xanrimi.

Haka kuma yayin da Sarki ya yi hawan Nassarawa, Xanrimi ne yake tafiya ya shaida wa Gwamna cewa Sarki yana tafe. Bayan wannan kuma aikinsa ne ya gabatar da hakimai a gaban Sarki don yin gaisuwa. Dukkan saqonninsu zuwa ga Sarki, ta hannunsa suke bi. Yayin da Sarki zai yi tafiya a mota, idan Shamaki baya nan, Xanrimi ne yake zama a gaban motar don riqe tagwayen masu. Har ila yau, shi ne yake shigar da maqaraya maza zuwa gaban Sarki yayin zaman fadanci. Kuma duk umarnin da aka bayar na shigo da wani ko wasu to alhakin Xanrimi ne ya shigo da su.



Bayan wannan kuma, Xanrimi na xaya daga cikin manyan bayin da suke riqe da 'ya'yan Sarki. Misali, ta fuskar xinke-xinkensu da sha'anin bukukuwa da kuma sa ido a kan gidajen da ake gina musu; shi ne kuma yake isar da saqonnin 'ya'yan Sarki zuwa ga Sarki, da kuma saqonnin Sarki zuwa ga 'ya'yansa. Haka ma abubuwan da suka shafi barorin Sarki da bayinsa ta hannun Xanrimi suke biyowa.

Haka kuma alhakinsa ne kula da dukkan gonakin Sarki (gandaye) a duk inda suke. Yayin da duk za a yi noma ko wani aiki da ya shafi gandayen, to alhakin lura da abin yana hannunsa. Duk lokacin da Sarki zai yi hawa, Xanrimi yakan aika a sanar da makaxa da mawaqan sarki da suke qarqashinsa irin su Sarkin Busa da Uban Kixi (sarkin taushi) da Sarkin Kotso da Magajin Banga da Sarkin Kuge da Sarkin Bambaxawa da Sarkin Kalangu da Sarkin Jauje da Soko da Kwandon Sarki da sauran su, da suke qarqashin sa ta hannun shugabansu, wato sarkin Busa, don su hawo su bi Sarki da kaxe-kaxe da bushe-bushe da waqe-waqe da sauran su (AIU 17/11/2005).

A lokutan hawa, duk wani umarni wanda ya shafi vangaren Xanrimi, to shi akan faxa wa, shi kuma sai ya sanar da wanda abin ya shafa don aiwatarwa. Har ila yau, dukkan raquman da 'yan tambura suke amfani da su, suna qarqashin kulawar Xanrimi. Shi ne mai kula da su ta fuskar cinsu da shansu da ma lafiyarsu. Duk wani abu da masu kula da raquman nan za su nema ta hannun Xanrimi suke biyowa.

Bayan wannan kuma, bisa al'ada a da, 'ya'yan Sarki raba su ake yi tsakanin gidajen manyan bayin Sarki. To shi ma Xanrimi yana daga cikin waxanda ake saka 'ya'yan Sarki a hannunsa, domin kula da al'amuransu. Dukkan wani abu da za su nema sai ta hannunsa da dai sauransu.

Kamar yadda bayani ya gabata a baya, Xanrimi yana da masu taimaka masa wajen gudanar da ayyukansa. Idan ka cire Makaman Xanrimi wanda Sarki ne yake zavarsa, sauran duk shi ne yake zavar sa, sai dai kawai ya nemi izni don tabbatarwa. Bayan waxannan hakimai nasa, akwai kuma waxansu sarautun da kuma yaran Sarki marasa muqami a qarqashin kulawarsa. Duk wani umarni da ya shafe su, ta hannunsa yake biyowa. Sarautun sun haxa da:

1. Sarkin Tafarki
2. Xansarai
3. Galadiman Zagi
4. Turakin Zagi
5. Sintalin Zagi
6. Makaman Zagi
7. Sarkin Takubba. (GZAL, 13/06/2005).

Ga bayanin ayyukan kowanne xaya daga cikinsu a taqaice domin samun qarin haske:



**Sarkin Tafarki**

Wannan shi ne shugaban mahaya 'yan sulke, waxanda suke a gaban sarki yayin da aka yi hawa, sanye da kayan yaqi cunkus cikin xamara ga kuma mashi, alhakinsa ne kula da adana kayan da ake amfani da su a lokutan hawa. Haka kuma shi ne yake tsara mahaya a layin sahu-sahu, yawanci biyar-biyar. Duk wani abu da ya shafe su ta hannunsa yake biyowa, alhakinsa ne kuma kula da lafiyar hanya a lokacin hawa.

**Xan Sarai**

Sarautar Xansarai sarauta ce ta barade tun zamanin ana yaqi. Ba shi da gurbi a lokacin fadanci, sai dai a lokacin hawa. A al'adance ba shi da wani aiki takamaimai da ya rataya a wuyansa. Xanrimi yana iya ba shi umarni don gudanar da wasu ayyukan (MDAMF. 08/08/2015).

**Galadiman Zagi**

Wannan shi ne na biyu a tsarin sarautar zagagen sarki, idan sarki yana tafe a qasa ko a kan doki, shi ne na biyu a jerin zagage. Ko yaushe yana xauke da wata alkyabba wacce take kunshe da wuqa da takobi, wuqar ita ce wacce sarki yake riqewa a hannunsa don karvar gaisuwa daga talakawa. Yayin da kuma yake rataya takobin. Alhakin Galadiman zagi ne ya sanya masa su yayin da duk ya buqata. Sannan kuma shi ne mai aiwatar da ayyukan Babban Zagi idan ba ya nan.

**Turakin Zagi**

Turakin Zagi shi ma ba shi da wani aiki da ya kevanta da shi. Sai dai duk lokacin da sarki yake tafe a qasa ko a doki yana cikin jerin zagage yana rataye da bargo a kafaxarsa da kuma sintali a hannunsa. Bayan haka kuma babban Zagi na iya umartar sa da ya gudanar da wasu ayyuka ko kuma riqe aikin wani idan ba ya nan.

**Sintalin Zagi**

Yana cikin jerin zagage, yana rataye da bargo a wuyansa ga kuma sintalin da ruwa a hannunsa. Ana tafiya da ruwan ne ko da buqata za ta taso. Misali alwala idan an sauka da makamantansu. Duk da cewa kusan kowane Zagi yana xauke da sintali da ruwa, Sarki ba ya amfani da sintalin kowa sai na Sintalin Zagi.

**Makaman Zagi**

Babban aikinsa shi ne kula da dokin sarki a lokacin da aka yi hawa, wannan ya haxa da gyaran shimfixa da linzami da likkafa da sauran su. Yayin da sarki yake tafe shi ma yana cikin jerin Zagage rataye da bargo da sintalin da ruwa a hannunsa.

**Sarkin Takubba**

Shi ma yana cikin jerin Zagage yayin da sarki yake tafe a qasa ko a doki. Shi ne shugaban Zagagen takubba. Suna cikin jerin Zagage xauke da takubba nannaxe a cikin fararen qyallaye, wani yana riqe da biyu wani na uku. Takubba ne masu tsohon tarihi



waxanda aka gada iyaye da kakanni. Takubba ne rantsattsu waxanda aka yi yaqe-yaqe da su (G2A/3/6/2015).

**Matsayin Sarautar Xanrimi A Masarautar Kano**

Babu shakka, sarautar Xanrimi da ma sauran manyan sarautun bayi daxaxxu ne a fadojin qasar Hausa. Kuma suna bayar da gagarumar gudummawa wajen tafiyar da al’amuran mulki a Kano.

A masarautar Kano, kafin a samar da majalisar Sarki, duk al’amuran mulki a hannun manyan bayin Sarki suke, kusan su ne manyan mashawartan Sarki. Abin nufi a nan shi ne suna da ruwa da tsaki wajen gudanar da masarautar Kano. Hakiman Sarki duk suna qarqashin kulawarsu. An kuma kasa su gida-gida. Misali akwai waxanda suke hannun Shamaki (Shamakawa) da waxanda suke hannun Xanrimi (Rimawa) da kuma waxanda suke gidan Salllama (Sallamawa) (MKASSY, 11/06/2005)

A wannan tsari, duk hakimin da yake da wani saqo ko koken al’ummarsa zuwa ga Sarki, to dole ne ya bi takan hakimin da yake hannunsa, domin cikinsu babu mai ikon zuwa ga Sarki kai tsaye ya gana da shi; saboda haka, a nan duk hakiman da suke qarqashin gidan Xanrimi, dole ne su biyo ta hannunsa idan suna da wani saqo zuwa ga Sarki. Haka kuma duk saqon da zai fito daga fada zuwa gare su, sai ya biyo ta hannunsa. A wancan lokacin Xanrimi yana xaya daga cikin manyan bayin Sarkin da ba sa halartar zaman fada, a inda Makaman Xanrimi yake zama a madadinsa. Amma a yanzu shi ne da kansa yake halartar

zaman domin gudanar da ayyukan da suka shafe shi (XKWN 080/06/2005).

Kafin zuwan Turawa qasar Hausa da kuma katin hana cinikin bayi, manyan bayin Sarki sun taka rawar gaban hantsi, yadda suke so. Sakamakon damar da suke da ita na kama bayi a lokacin yaqe-yaqe. Domin kuwa, duk yayin da aka tafi yaqin faxaxa iyakar qasa, komai yawan bayin da waxannan barade suka kama nasu ne, su suke da ikon yin duk abin da suka ga dama da su. Ma’ana, su sayar ko kuma su bautar da su. Xanrimi a matsayinsa na babban bawan Sarki yana daga cikin manyan jami’an tsaro, wato kafin a samar da ’yan Doka da ’yan Sanda.

Babu shakka, Xanrimi yana da matuqar tasiri da kwarjini a masarautar Kano, domin abubuwa da dama ba sa yiwu wa sai da sa hannunsa, matsayinsa kuma a tsakanin al’umma babba ne, saboda ana tsoron sa ana kuma girmama shi. Har yanzu kuwa ruwa yana maganin dauxa, domin duk da cewa an samu ’yan sauye-sauye da suka raunana tasiri da tsarin sarautar gargajiyar kanta, har yanzu sarautar Xanrimi ba qaramin matsayi da tasiri take da shi ba a fada da ma idanun sauran al’umma. Kuma har kwanan gobe ana ganin abubuwa da dama na gudanar da mulki ba za su tafi yadda ya kamata ba, ba tare da sa hannunsa ba, musamman ma idan aka yi la’akari da ximbin ayyukan da yake gudanarwa a ciki da kuma wajen fada. Sauran al’umma suna ganin girman sarautar Xanrimi, suna kuma martaba mai riqe da ita (IAU, 04/06/2005).



**Kammalawa**

Babu shakka Sarautar Xanrimi muhimmiyar sarauta ce a tsakanin sarautun manyan bayi, hasalima ita ce ta biyu a fuskar muqami. Muhimmancinta wajen gudanar da al’amuran da suka shafi mulki abin la’akari ne, shi ne ya sa wannan takarda ta dubi alfanun yin tsokaci a kanta.

A qarshe, ina fata wannan takarda za ta amfani xalibai ’yan’uwana da malamai da ma sauran jama’a masu sha’awar wannan muhimmin fage, tare da kasancewarta wata hanya ta adana kyawawan al’adun Hausawa waxanda aka gada iyaye da kakanni.

**Manazarta**

Abubakar A. S (2008) Sarautar Sallama da ta Sarkin Hatsi a Fadar Kano. Kundin Digiri na Biyu. Sashen Koyar da Harsuna, Jami’ar Bayero, Kano.

Adamu M. W (1998) Qwaraqwarai a Fadar Kano. Kundin Digiri na Xaya. Jami’ar Bayero, Kano.

Ahmad M. G (2001) *Tarihin Sarakunan Kano 1805 – 2003* Kano Triumph Publishing Company.

Anold, S. S (1999) The Kano Mamluks: Royal Slavery in Sokoto

Caliphate (1807 – 1903). Kundin Digiri na Uku. Jami’ar Bayero, Kano.

Bargery, G. P (1934) *AHausa English Dictionary*

Bello A. S (1991) Tasirin Zuwan Turawa kan Sarautun Gargajiya na

Qasar Hausa. Kundin Digiri na Biyu. Jami’ar Bayero, Kano.

Inuwa M. M (1997) Sarautar Sarkin Dogarai a Garin Kano. Kundin Digiri na Xaya, Jami’ar Bayero, Kano.

Isma’il M. (1986) Tsarin Sarautar Gargajiya Jiya da Yau. Kundin Digiri na Xaya, Jami’ar Bayero, Kano.

Saleh G. (2006) Sarautar Shamaki da Xanrimi a Masarautar Kano. Kundin Digiri na Biyu, Jami’ar Bayero, Kano.

Mahmoud A. A (2002) Sarautu a Masarautar Kano. Kundin Digiri na Xaya, Jami’ar Bayero, Kano.

Sufi, A. H. (1993) *Mu San Kanmu:* Mai-Nasara Press, Kano.

Suleiman A. H. (1981) Fada da Jami’anta. Kundin Digiri na Xaya, Jami’ar Bayero, Kano.

Zhenghong, M. (1985) Tsarin Mulkin Gargajiya a Qasar Hausa. Kundin Digiri na Xaya, Jami’ar Bayero, Kano.

**Mutanen Da Aka Yi Hira Da Su**

Babban Zagin Sarkin Kano Alhaji Garba (BZSKAG), 28 - 03 1996.

Ciroman Shamaki Kabiru Inuwa (CSKI), a ranar Litinin 20/04/2005 a kamfanin Mai na Nigeria Oil Mills, Limited, Kano.



Xanrimin Kano Wada Najolo (XKWN), a ranar Laraba 08/06/2005. a gidansa da yake cikin gidan Sarki, Qofar Qwaru.

Galadiman Zagi Alhaji Ibrahim (GZAI), a ranar 13/08/2005, a gidansa da yake Qofar Qwaru.

Hasken Fadar Sarkin Kano, Alhaji Bala (HFSKAB), a ranar 07/06/2005, a Qofar Na’isa Hauren Motoci.

Ibrahim Abdullahi Usman (IAU), a ranar Juma’a 04/06/2005, a gidansa a Unguwar Sagagi.

Makaman Xanrimi Alhaji Mustapha (MDAM), a ranar Laraba 08/06/2005, a Unguwar Rimin Qira.

Madakin Kano Abdullahi Sani Sarki Yola MKASSY, a ranar 11/06/2005, a gidansa da yake Unguwar Yola.

Shamakin Sarkin Kano Alhaji Inuwa (SSKAI), a ranar Laraba 08/06/2005, a gidansa da yake cikin gidan Sarki.

Umaru Kurawa (UK), a ranar Laraba 15/06/2005 a gidansa da yake unguwar Kurawa.

Wamban Katsina Muhammadu Gixaxo Abba Kalli (WKMGAK), a ranar Juma’a 12/08/2005, a gidansa da yake Katsina. Lambun Wambai, Katsina.

Wakilin Tarihi na Masarautar Daura Mamman Siya Abubakar (WTMDMSA), a ranar Alhamis 11/08/2005, a fadar Sarkin Daura, Daura.